# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Haihuwar Yesu



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: M. Maillot**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: E. Frischbutter; Sarah S.**

**Fassarawa: Maren Dameng Daniel**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2023 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**


Da jimawa, Allah ya aiko mala’ika Jibrilu, zuwa ga wata budurwa mai tagomashi mai suna maryamu cewan “zaki haifi ɗa zaki ƙira sunansa Yesu. Za’a ƙira shi madaukaki.
Zai yi mulki har abada.”

“Yaya hakan zai kasance?”
Maryamu ta yi tambayan.
“Ban taɓa sanin namiji
ba” mala’ika yace
wa maryamu, ɗan
cikinki daga wurin
ubangiji ne.  Ba
zai kasance da
uba mutum ba.



Mala’ika ya faɗa wa Maryamu cewan 'yar uwarta Alisabatu cikin tsufanta tana da ɗa a cikin ta. Wannan ma abin mamaki ne. Nan kaɗan Maryamu ta ziyarci Alisabatu. Suka yi farin ciki tare.



Maryamu na da alkawarin aure wani mutum mai suna Yusufu. Yusufu yayi baƙin ciki lokacin daya ji cewan Maryamu zata haifa ɗa. Yana zaton cewan wani mutum ne baban yaron.



A cikin mafarki, malaikan ubangiji ya faɗawa Yusufu cewan wannan ɗa daga Allah ne.  Yusufu ne zai taimaki Maryamu lura da Yesu.



Yusufu ya gaskata ya kumayi biyayya ga Allah.  Yayi biyayya ga dokan ƙasarsu. Saboda sabuwar doka, shi da Maryamu



sun tafi

ƙasarsu baitalami, don su biya harajinsu.



Maryamu ta shirya ta haifi ɗanta. Amma Yusufu bai sami daki a ko'ina ba. Dukan

wurare sun cika.

A karshe Yusufu ya sami wuri. A wannan wuri aka haifi Yesu. Mamansa ta kwantar dashi a kan saƙarƙai, wurin da ake saka wa dabbobi abinci.




A kusa kuma makiyayan da suke a wurin suna lura da dabbobin su dake bacci. Mala’ikan ubangiji ya bayyana,
ya fada masu sabuwar labari mai dadi.


“Yau an Haifa maku mai ceto cikin birnin
Dauda shi ne mai ubangiji
ceto. Zaku sami
ɗan an
kwantar
da shi akan
saƙarƙari.”


Nan da nan, mala’iku sun bayyana,
suna yabon Allah suna cewa,
“Daukaka ga Allah a
cikin suna
mafi
daukaka ga
Allah, salama
ga duniya, jalla
ga jama’a.”


Makiyaya sun hanzarta zuwa masauƙin.
Bayan sun ga yaron sun faɗa ma kowa
da suka haɗu dashi abinda malaiƙu
suka faɗa game da Yesu.


Bayan kwana arba’in, Yusufu da Maryamu sun kawo Yesu cikin haikali a urisharima.  A nan wani mai suna siminu ya yabi ubangiji domin wannan yaro sai wani bawan ubangiji mai suna Anna ya nuna gadiya.



Dukkansu sun gane Yesu
ɗan Allah ne, mai ceto
da aka alƙawarta.
Yusufu ya yi
hadayan tsuntsaye
biyu wannan
shi ne baiko da
dokokin ubangiji
ta umurta talaka
ya kawo yayin da
ya miƙa yaronsa
a ikklissiya.



Ba'a jimaba, wata tauraro na musamman ta yi wa shehuna daga gabas jagora zuwa birrin urishalima. “Ina sarkin yahudawa da aka Haifa?” suka tambaya “Muna so muyi masa sujada.”



**Sarkin Hirudus ya ji labarin shehuna da suka zo daga gabas. Ya damu kwarai, ya ce masu, idan sun je sun ganshi sai su zo su fada masa don shi ma yanaso ya je ya yi ma wannan sabon sarki sujada. Hirudus yana so ya kashe Yesu ne.**





Tauraro ya yi wa shehunan jagora har zuwa wurin da Maryamu da Yusufu suke tare da Jaririn. Suka durƙusa da gwuiwan su a ƙasa, suka yi masa sujada, waɗannan matafiyan suka bada manyan kyautuka ga Yesu na zinariya da turare masu ƙamshi.

Allah ya kwaɓi
shehunan cewan
su koma a ɓoye.
Hirudus ya fusata.



Ya shirya ya kashe Yesu, mai mulkin ya yi umurnin kisan duk Jarirai maza a cikin Baitalami.



Amma Hirudus bai iya hallaka ɗan Allah ba!  A cikin mafarki ubangiji Allah ya kwaɓi Yusufu ya ɗauki Maryamu da Yesu ya boye su a masar.





Lokacin da Hirudus ya mutu sai Yusufu ya dawo da

Maryamu da Yesu daga masar.  Suka yi zama a kasar Nazaret, kusa da tekun Galili.

# Haihuwar Yesu

## Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

## a na samu a

## Matta 1-2, Luka 1-2

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**

# KARSHE

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah: Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**